# Littafi mai Tsarki na yara
## Ke gabatar da



# Mutum da aka aika daga Allah

Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: Byron Unger; Lazarus
Alastair Paterson

Mai niyyan daukan nauyi: E. Frischbutter; Sarah S.

Fassarawa: Bible Society Nigeria

Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org

©2024 Bible for Children, Inc.
Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.



Wata rana a cikin haikalin Allah, wani tsohon firist, mai suna Zakariya yana konna turare. A waje, mutane suna addu'a. Nan da nan, Zakariya ya fara rawar jiki.




Mala’ika ya riga ya zo. “Kada ka ji tsoro,” ya ce. “Allah ne ya aiko ni. Matar ka za ta haifi da namiji. Ka ba shi suna Yohanna. Za a cika shi da Ruhu Mai Tsarki daga haifuwa. Zai dawo da mutane da dama zuwa ga Allah.”
3


“Ka yi magana da mu, Zakariya.” Mutanen da suke waje suna ta rasa gane abin da ke faruwa. Ba su sani cewa mala’ika Jibirellu ya gaya wa Zakariya cewa ba zai iya magana ba har sai an haife jaririn domin ya ki ya ba dagaskiya ga sakon Allah ba. Yana tunani cewa matarsa ta tsufa kuma ba za ta iya haifuwa ba.
4


A gida, Zakariya ya rubuta duka abin da mala’ikan ya fada masa. Alisabatu, matarsa, ta yi mamaki. Kullum suna ta roko a ba su yaro. Zai iya faruwa yanzu?
5


Ba da daddewa ba Alisabatu ta sani cewa yaro na zuwa. Sai ta yabi Allah. Wata rana, ‘yar’uwar Alisabatu na dangi Maryamu ta ziyarce ta. Ita ma Maryamu tana da ciki.
6


Sa’ad da Maryamu ta kai wurinta, Alisabatu ta ji jaririn ya yi tsalle a cikinta. Alisabatu ta cika da Ruhu Mai Tsarki. Sai ta sani cewa yaron Maryamu ne zai zama Ubangiji Yesu Kiristi. Tare, su biyu suka yabi Allah cikin farin ciki.
7


An haifi yaron Alisabatu kamar yadda Allah ya yi alkawari. “A kira shi Zakariya kamar babansa,” sauran firistocin suka ce. Zakariya kuwa ya tuna da umurnin Allah. “A’a! Sunan yaron shi ne Yohanna.” Sa’ad da Zakariya ya rubuta wadannan kalmomin, sai iya maganarsa ya dawo masa. Sa’an nan ya yabi Allah.
8

Lokacin da Yohanna ya yi girma sai ya zama kamar Iliya, jarumi mutumin Allah. Yohanna ya gaya wa mutane cewa ba da daddewa ba Mai Ceto zai zo don ya albarkace su. Shugabanin Yahudawa sun tsani Yohanna domin ya ce musu, “Ku Tuba! Ku bar yin zunubi.” Ba su so su ji kome game da zunubansu.



9

Wadansu sun kira shi Yohanna mai Baftisma domin ya lume mutane cikin ruwa domin su nuna cewa sun tuba daga zunubansu. Wata rana, Yesu ya zo wurin Yohanna domin a yi masa baftisma. “Yakamata kai ne ka yi mini baftisma,” Yohanna yana ki. Amma Yesu ya ce, “Bari ya kasance haka.” Sai Yohanna ya yi masa baftisma.



10

Bayan baftismar Yesu, Yohanna ya ga Ruhu Mai Tsarki yana saukowa a kan Yesu kamar kurciya. Wannan ita ce alama daga Allah. Yohanna ya sani cewa Yesu dan Allah ne. Yohanna ya kira Yesu dan tunkiya na Allah wanda yake kawar da zunuban duniya.



11



Yohanna ya kai mutane da dama zuwa wurin Allah. Amma Hirudus, shugaba mai mugunta, ya jefa Yohanna a kurkuku. “Zunubi ne ka auri Herodiya matar dan’uwanka ta zama matarka.”

12



Yohanna ya fada wa Hirudus. Hirudus ya sani cewa wannan gaskiya ne. Ya sani cewa Yohanna dan hidiman Allah ne, mutumin kirki da tsarki. Amma ba ya so ya bar yin zunubi ba. Kuma Yohanna ba barin yin wa’azi a kan zunubi zai yi ba, ko da ma za a sa shi a kurkuku.

13

A ranar tuna da ranar haifuwarsa, sai ya yi babban biki. ‘Yar Herodiya ta yi masa rawa. Wannan ya faranta masa rai. “Za ki tambaya duk abin da ranki yake so,” ya yi alkawari. “Ko da ma rabin kasar da nake mulki ne.”



14



"Mene ne zan tambaya?" yarinyar tana tunani. Sai muguwar mahaifiyarta, wadda ta tsani Yohanna, ta gaya mata abin da za ta tambaya. Ba abu mai dadin ji ba ne.

15

"Ka ba ni kai na Yohanna Mai Baftisma a kwano," yarinyar ta gaya wa Hirudus. Sai bai ji dadin alkawarin da ya yi ba, amma saboda girman kai ya ki ya canja alkawarin. "Ku yanke kan Yohanna ku kawo shi a nan," ya ba da umarni. Sojojinsa suka yi biyayya gare shi.



16

Abin bakin ciki abokan Yohanna suka bizne jikin dan hidima na Allah mai karfin hali da mai aminci.



17

Mutum da aka aika daga Allah

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Markus 6, Luka 1, 3

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130

18




37 60

19

Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin
Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.

Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.

Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:
Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.

Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16

20